**[1]Lawi Yusuf, [2]Nura Musa Jamilu, [3]Sadiq Abubakar Bello and [4]Safiyanu Aminu Salihu**
[1]Department of Languages and Linguistics, University of Maiduguri.
[2&3]Department of Hausa, College of Education Zing, Taraba State
[4]Department of Languages and Linguistics, Taraba State University, Jalingo

# Siddabaru a Rayuwar Al'ummar Hausawa ta Yau: Nazarin Sigogi da Tasirinsa

**Tsakure**

Wannan bincike mai taken "Siddabaru a Rayuwar Al'ummar Hausawa ta Yau: Nazarin Sigogi da Tasirinsa" ya yi nazari ne kan yadda siddabaru ke bayyana a rayuwar Hausawa ta zamani tare da fayyace manyan sigoginsa da tasirinsa a zamantakewa. Manufar aikin ita ce gano sigogin siddabaru da yadda yake tasiri ga al'umma a yau. An yi amfani da ra'inRufa-Ido (Illusion Theory) domin bayyana yadda siddabaru ke kasantuwa a wurin al'umma da sauye-sauyen zamani, don rai'in ya karkata ga yadda mutane ke ganin abubuwa ba daidai da yadda suke ba, saboda galibi Siddabaru yana ginuwa ne a kan yaudarar gɓani da fahimta. Binciken ya yi amfani da hanya mai inganci inda aka bi hanyoyi uku wajen tattara bayanai da aka yi amfani da su a cikin wannan takarda da suka haɗa da: Ganawa da mutanen da ake neman bayanai a gare su. An yi amfani da salon gani da ido. Wanda aka je fagen da suke gudanar da siddabaru, aka ga yadda suke bajewa da yadda suke gudanarwa a cikin al'umma, sai hanyar karantawa daga rubutattun bayanai, inda aka karanta bayanan da suka danganci abubuwan da suka shafi siddabaru. Bayan gudanar da nazarin, sakamakon bincike ya nuna cewa siddabaru yana bayyana a matsayin nishaɗi, dabara a tallace-tallace da kasuwanci, da kuma hanyar yaudara a wasu lokuta musamman a kafafen zamani. Binciken ya kuma nuna cewa siddabaru na taimakawa wajen bunƙasa fasaha da ƙirƙira, amma yana iya haifar da ruɗani idan aka yi amfani da shi ba da gaskiya ba.

**Muhimman Kalmomi: Siddabaru, Sigogi, Rufa-ido, Sihiri**
**Received**: 04/07/2026 Accepted: 31/07/2026 GSM: +2348036115097/+2348145067620
**Corresponding Author**: Yusuf, L. **Email:** hajaraumarlawi@gmail.com
**Article Citation**: Yusuf, L., Jamilu, N. M., Bello, S. A. and Salihu, S. A. (2026). Siddabaru a Rayuwar Al'ummar Hausawa ta Yau: Nazarin Sigogi da Tasirinsa. *Jalingo Journal of Languages and Literary Studies (JAJ0LLS). 10 (2) pp.190-198*
**Publishers**: Department of Languages and Linguistics, Taraba State University, Jalingo.
**ISSN**: 2488-9067

## Gabatarwa

Akasarin rayuwar Bahaushe wanda ta ƙunshi tun zuwarsa duniya har komawarsa ga Allah, tana ƙunshe da wasu abubuwa da ake ganin su ne al'adunsa da ɗabi'unsa da tunane-tunanesa da tarihinsa da sana'arsa da harshensa wanda da shi ne ake gane halin da yake ciki da muhallinsa da addininsa da duk wani abu da ya shafi rayuwarsa ta duniya da ta zamani. Wani muhimmin al'amari daga ciki da ke nuna yadda ɗan Adam ke iya kuskure wajen fahimtar abin da yake gani ko ji shi ne Siddabaru. Siddabaru wani tsohon al'amari ne da ya ginu a kan nuna bajinta, tsubbu, ɓoyayyen ilimi, ko kuma dabarun tafi-da-gidanka waɗanda suke ba wa mai yin sa damar aiwatar da

abubuwan da suka saɓa wa hankali ko saɓa wa yanayi na zahiri. A rayuwar yau da kullum, mutane suna fuskantar siddabaru ba tare da sun sani ba. Wannan ya sa masana suka mayar da hankali wajen nazartar yadda kwakwalwa ke fassara bayanai daga muhalli. Wannan bincike zai yi bayani dalla-dalla a kan siddabaru domin fahimtar asalinsa da tasirinsa.

**Ra'in Rufa-Ido (Illusion Theory)**

Ra'in Rufa-Ido (Illusion Theory) wani ra'i ne da ke bayyana yadda hankalin ɗan Adam ke iya fassara wani abu ba daidai da yadda yake a zahiri ba. Wannan na faruwa ne idan idanu ko sauran gaɓoɓin ji suka karɓi wani saƙo, amma ƙwaƙwalwa ta fassara shi ta wata hanya dabam. Saboda haka, mutum yana ganin ko fahimtar wani abu daban da ainihin abin da yake faruwa. Shi wannan ra'i na Rufa-Ido ya samo asali ne daga fannin ilimin tunani (Psychology), musamman nazarin yadda mutum ke gani da fahimtar abubuwa. Masana irin su Hermann ɓon Helmholtz da Richard Gregory (1987) sun yi bayanai kan yadda kwakwalwa ke yin hasashe da fassarar abin da idanu suka gani, wanda wani lokaci kan haifar da kuskuren fahimta. Ra'in ya ginu ne a kan wasu muhimman ginshiƙai kamar haka:

i. Akwai abin da ake gani a zahiri, amma ba lallai ne a fahimce shi yadda yake ba.
ii. Ana iya yaudarar gani da fahimta ta hanyar amfani da wasu dabaru na musamman.
iii. Tunanin mutum da abin da ya saba gani na iya rinjayar fahimtarsa
iv. Kwakwalwa tana fassara bayanan da take samu daga idanu, kuma wannan fassarar na iya zama kuskure.
v. Muhalli da yanayin da mutum yake ciki na iya tasiri wajen yadda yake fahimtar abin da yake gani.

Ra'in Rufa-Ido ya dace matuƙa da wannan binciken, dalilin haka kuwa shi ne siddabaru galibi yana amfani da dabarun da ke sa mutum ya ga wani abu daban da abin da ke faruwa a zahiri. Mai siddabaru kan yi amfani da saurin motsi, karkatar da hankali, ɓoye wani abu, ko amfani da wasu hanyoyi na ruɗar gani domin sa masu kallo su yi kuskuren fahimtar abin da suke gani. Misali:

i. Ɓoye wani abu a gaban jama'a ba tare da sun lura ba.
ii. Fitar da tsuntsu daga kwalin da babu komai a ciki.
iii. Mayar da takarda ta zama kuɗi.
iv. Nuna mutum kamar ya ɓace ko ya canja wuri cikin sauri.

Duk waɗannan misalai suna nuna yadda siddabaru ke amfani da rufa-ido wajen yaudarar gani da fahimtar masu kallo.

**Amfanin Ra'in ga Binciken**

Wannan ra'in zai taimaka wajen:

i. Gano sigogin siddabaru a rayuwar Hausawa.
ii. Bayyana yadda siddabaru ke aiki ta fuskar gani da fahimta.
iii. Nazarin tasirin siddabaru ga tunani da ɗabi'un al'umma.
iv. Bambance siddabaru da sihiri ko tsafi ta fuskar ilimin tunani.
v. Fahimtar dalilan da ke sa mutane su gaskata ko su yarda da siddabaru.

**Hanyoyin Gudanar da Bincike**

A wannan bincike an bi hanyoyi uku wajen tattara bayanai da suka sahfi wannan takarda da suka haɗa da:

i. **Hira**: An gudanar da hira da wasu masu siddabaru, masana al'adun Hausawa, da dattawan al'umma domin jin ra'ayoyinsu kan siddabaru, sigoginsa, da tasirinsa a yau. An yi amfani da hira mai ɗauke da tambayoyidomin ba mahalarta damar yin cikakken bayani.

https://doi.org/10.66490/jajolls.2026.v10.i2.018

ii. **Lura Kai Tsaye**: Mai bincike ya halarci wasu wuraren da ake gudanar da siddabaru domin lura da: Hanyoyin gudanar da siddabaru da Kayan aikin da ake amfani da su da Mu'amalar masu siddabaru da masu kallo da Yadda jama'a ke karɓar siddabaru.

iii. **Karantawa daga rubutattun bayanai**: Daga ƙarshe, an gudanar da wannan bincike ta hanyar karantawa daga rubutattun bayanai, inda aka karanta bayanai daban-daban da suka shafi siddabaru, sihiri, tsafi, rufa-ido, da al'adun Hausawa domin ƙarfafa bayanan da aka samu daga fage a cikin littattafai da kundayen bincike da aka gudanar a Jami'o'i. Haka kuma, an samo wasu bayanai da aka gabatar, a tarurrukan ƙara wa juna sani.

**Ma'ana da sharhi kan siddabaru**

A ɓangaren lugga, kalmar siddabaru, kamar yadda Bargery (1934) ya nuna Siddabaru, tana nufin dabo. Shi kuma Ƙamusun Hausa (CNHN, 2006) ya nuna kalmar siddabaru ita ce, "wasu dabaru na sihiri waɗanda suka wuce fahimtar hankalin ɗan'adam", sannan kuma kalmar siddabaru tana iya zama dabo ko rufa-ido.

Idan aka kalli kalmar siddabaru ta fanni ilimi kuwa, masana al'ada da rayuwar ɗan'adam sun bayyana ta ta fuskoki daban-daban. A wata ma'ana ta isɗilahi kalmar siddabaru tana nufin dabaru na cukurkuɗa abubuwa da rikirkita su tare da ɓatar da bakin zare har a kasa gane lissafi (Bunza, 2024). Wani lokaci kuma tana nuni a kan wayo da dabara wajen kare kai ko kuɓutar da kai tare da yin layar zana. (Gobir, 2022). Wasu kuma suna ganin, siddabaru ya ƙunshi yin surkulle da ɓatar da sau da kau da gani a samar da abubuwa ko a gudanar da wasu ayyuka na ban mamaki. (Gusau, da Funtua, 2021).

Don haka, siddabaru yana nufin sanin yadda za a yi wasa da hankalin mutum har ya yi mamakin yadda abubuwa ko ayyuka suka faru. A wannan madosa za a daɗa faɗaɗa ilimin siddabaru ya haɗa da fasaha da azanci da rufa-ido da surkulle da dabo da sihiri da saɓa-al'ada da makamantar waɗannan abubuwa. Ta waɗannan hanyoyi ne ake yin siddabaru da cakuɗe-cakuɗen abubuwa domin a gigitar da hankalin mutane ta yadda duk mutum ya kai da wayo ko ganewa sai an shigar da shi duhu.

**Siddabaru a Matsayin Ilimi**

Idan aka yi la'akari da yadda aka bayyana ma'anar ilimi, musamman kamar yadda Ƙamusun Hausa ya nuna, ilimi shi ne sani ko ganewa ko fahimta (CNHN, 2006), to, Siddabaru wani ilimi ne na musamman wanda ba za a iya aiwatar da shi ba sai an fahimci dabaru da hanyoyin gudanar da shi. Dabaru na gigitar da hankali da cukurkuɗa tunanin mutum dole ne sai an nemi sani na yin su, in ko ba haka ba, sai a faɗa rijiya da baya.

Ilimin siddabaru ya ƙunshi hanyoyi na amfani da wasu surkulle da rufa-ido da ɓad-da-sawu da fyauce hankali da tafi-da-gani domin a cim ma maƙaryar zakuɗa hankalin mutum a dame masa lissafi. Ta haka kuma siddabaru zai kai ga samun sakamako na gudanar da shi.

A ilimin siddabaru har wa yau, babu wata hanya guda ɗaya rak wadda ta zama dole sai ta kanta za a iya aikata shi. Akwai hanyoyi da yawan gaske waɗanda za a iya ɓullowa da su a ilimin siddabaru waɗanda kuma za su iya bambanta a tsari da yanayi na tafiyar da su, (Bunza, 1990)

**Tarihin Ilimin Siddabaru a Al'ummar Hausawa**

Adamu, (1990), Allah, mai girma da daukaka, ya hore wa al'umma hanyoyi na sarrafa tunani su dinga sama wa kansu dabaru na zaman rayuwa. Haka kuma ya lakanta musu hikimomi da azance-azance wadanda suke yi wa al'ummu jagoranci wajen tafiyar da tunanin nasu da yake ba su damar kullawa da kwance abubuwa. Siddabaru da sihirce-sihirce wasu abubuwa ne wadanda, kamar yadda aka nuna a baya, suke gudana ta hanyar tunani da azanci. Ire-iren Waɗannan abubuwa da tunani yake yi wa jagoranci sukan zama tawayu ga al'umma kuma su kasance sarke da rayuwarta tun a tumun fari.

Ilimin Siddabaru a wajen Hausawa abu ne mai dadadden tarihi wanda Hausawa suka same shi daga haujin kansu tun a rayuwarsu ta zaman farko. Tun a rayuwa ta maguzanci, Hausawa a mabambantan hanyoyinsu na tunani da samar da abubuwa, suka kirkiri aiwatar da wasu dabaru na yin abubuwa da za su ba da mamaki ko su daga hankali ko shashantar da matakan lura da tantancewa wadanda aka dauka siddabaru ko sihiri ne.

Tun a lokacin da Hausawa suka fara farauta ta tudu da ta ruwa da yawace-yawace a dazuzzuka suna neman 'ya'yan itatuwa da tariyar namun daji gaba-gaba domin samun abinci suka sami dabaru na siddabaru da sihirce-sihirce na kariyar jiki. Ta haka suka fara sama wa kansu matakai na kare rayuwarsu daga wasu halittu waɗanda suka fahimci masu cutarwa ne a gare su.

Haɗuwar Hausawa da al'jannu ta hanyar addinin gargajiya na bautar iskoki da dodonni ya ba Hausawa wata mayalwaciyar dama su daɗa bunƙasa matakai na yin siddabaru, musamman yadda wasu iskoki suke taimaka wa Hausawa wajen tafi-da-gani na mutane. Ta haka bori da tsafe-tsafe da sauran abubuwan da suka shafi addinin gargajiya suka ba wasu Hausawa damar zarmewa a wajen aikata abubuwa masu ba da mamaki.

Hulɗoɗin rayuwar Hausawa a wajen tafiyar da abubuwa na bukatun rayuwarsu kamar sana'o'i na kyautata tattalin arziki da bukukuwa na ƙara yauƙaƙa rayuwa da wasanni na kyautata jiki da ƙwaƙwalwa da kaɗe-kaɗe da waƙe-waƙe na yi wa rai yayyafi da nusarwa sun tattaimaka wajen daɗa faɗaɗa matakai na yin abubuwan siddabaru da sihiri da kau-da-ido.

A kowane rukuni ɗaga cikin waɗannan rukunoni na tafiyar da rayuwa akan sami wasu mutane waɗanda a ayyukansu za su yi ta ƙokarin yin wasu abubuwa domin su ba da mamaki ko don burgewa ko don fito da ƙwarewarsu da nuna matuƙar azanci nasu. A wajen yin haka ne suke tafiyar da hankali na mutane ko su sace fahimtarsu ko ganewarsu, ɗaga nan ne asalin siddabaru.

Duk da zuwan addinin Musulunci a ƙasar Hausa da shigar sa lungu-lungu, siddabaru ya shiga a tunanin wasu Hausawa waɗanda suka ci gaba da gudanar da abubuwa na ban mamaki a kaikaice wasu lokuta har da neman taimako ɗaga aljannu wato iskoki.

Ma'amalar Hausawa da magungunan gargajiya domin neman waraka daga cututtuka da bokaye da 'yan bori da sauransu suka yi fice wajen badawa, ita ma hanya ce wadda ta daɗa haɓakawa da yin dabdala ta yin siddabaru. Waɗannan masu ba da magunguna sun ɗauki siddabaru wata hanya wadda za ta ƙara sanya a amince da magungunan da suke badawa. Ta haka sai su dinga yin abubuwa na ɗaga hankali da kawar da tunani amma ta hanyar siddabaru.

A dunkule, ilimin siddabaru, ilimi ne wanda Hausawa suka ƙirƙire shi da kansu tun a lokaci daɗaɗɗe na rayuwarsu ta gargajiya, sannan ya ci gaba da bunƙasa a lokacin da Hausawa suka dinga nuna dabaru na buwaya da nuna ƙwarewa da kuma nuna fifikon fasaha da gwaninta a tsakanin masu ayyukan bajinta ko sana'o'i da sauran ma'amaloli. Haka kuma siddabaru ya ƙara samun ranar shanya gari a lokatan da Hausawa suka dinga hulɗoɗi da baƙin al'ummu har suka sami fannoni ilimi iri-iri har gami da ilimi na tafi-da-hankali, musamman bayan zuwan addinin Musulunci da fahimtar ilimin Larabci da na shari'a. Ga kuma zuwan Turawa da Indiyawa da Fulani da Barebari da Yarbawa da Igbo da sauransu.

Bayan Hausawa sun yi nisa cikin wannan cuɗanya da ma'amaloli kuma sun sami ilimi na addinin Musulunci da na boko, sai suka shiga rarrabe siddabaru a matsayin dabaru na kawar da ido ko rufa-ido ko tawalwaniya ko sihiri ko tsafi ko surkulle ko kuma wasu dabaru na ɗauke hankalin mutum.

**Ire-iren Siddabaru na Hausawa**

Akwai hanyoyi daban-daban, kamar yadda aka nuna a baya waɗanda ake bi ta kansu ana gudanar da siddabaru a al'ummar Hausawa. Daga cikin ire-iren hanyoyin akwai:

1. Sihiri ko tsafi

https://doi.org/10.66490/jajolls.2026.v10.i2.018

2. Rufa-ido
3. Surkulle
4. Dabo
5. Damfara
6. Bori

**Sihiri**:

Na nufin amfani da wasu hanyoyi na boye ko dabaru domin yin tasiri a kan mutane, abubuwa ko al'amura ta hanyar da ta saba da yadda aka saba gani ko fahimta. A al'adu da addinai da dama, ana kallon sihiri a matsayin aiki da ke amfani da karfi na boye, aljanu, tsafe-tsafe, ko wasu dabaru domin cimma wata manufa. (Bunza, 2021)

**Rufa-ido**

Kalma ce ta Hausa da ke nufin yaudara, ruɗi, ko ɓoye gaskiya domin a sa mutum ya kasa gane hakikanin al'amari. Ana amfani da ita a zahiri da kuma a ma'ana ta salon magana. (Bunza, 2021)

**Surkulle**

Na nufin dabara mai rikitarwa, ruɗani, ko wani yanayi da aka ƙulla domin ɓoye gaskiya ko wahalar da fahimta**.** Kalmar tana ɗauke da ma'anar rikicewa, ƙulli, ko wahalar gano hakikanin abu. (Bunza, 2021)

**Dabo**

Na nufin dabara, wayo, ko wata hikima da ake amfani da ita domin cimma wata manufa cikin sirri ko salo na musamman**.** A wasu lokuta, kalmar tana iya ɗaukar ma'anar yaudara ko salon kauce wa gaskiya. (Bunza, 2021)

**Damfara**

Na nufin yaudara ko zamba da ake yi domin cutarwa ko karɓar abin wani ta hanyar ruɗi da rashin gaskiya**.** Ana danganta damfara da cin amana, zamba cikin aminci, ko amfani da wayo mara kyau domin anfani da wani. (Bunza, 2021)

**Bori**

Tsohuwar al'ada ce a cikin al'ummar Hausawa wadda ta shafi tsafi, camfi, kiran iskoki, da wasu ayyuka na gargajiyada ake dangantawa da aljanu ko ruhohi. A wasu lokuta ana kallon bori a matsayin hanyar neman magani, kariya, ko warware matsaloli ta hanyar amfani da ikon iskoki. (Bunza, 2021)

**Mahaɗin Siddabaru**

A wajen gudanar da ayyuka na siddabarun Hausawa Adamu, (2020) y ace akwai wasu abokan haɗi waɗanda sukan taimaka a sami harhaɗa dabarun cikin sauƙi da daidaito. Waɗannan abubuwa su ne aka kira matallafan gudanar da siddabaru waɗanda kuma suka haɗa da dabbobi da tsuntsaye da ƙwari da halittun ruwa da itatuwa da tsirrai da dauwarwatsu da gulabe da dazzuzzuka da kushewu da rumbuna da yashi da makamantansu.

Daga cikin dabbobi, akwai dabbobi na gida kamar rago da tinkiya da akuya da doki da jaki sauransu. Akwai kuma dabbobi na daji, misalin giwa ko zaki ko ɓauna ko ƙura ko dila da makamantansu.

**Siddabaru a Rayuwar Al'ummar Hausawa da Sigogin ta a Yau**

Siddabaru a yau yana bayyana ta fannoni daban-daban kamar haka:

**a. Siddabarun Kasuwanci**

i. Yaudara wajen sayar da kaya
ii. Rage ingancin kaya amma a nuna suna da kyau
iii. Talla ta ƙarya

https://doi.org/10.66490/jajolls.2026.v10.i2.018

**b. Siddabarun Siyasa**

i. Alkawuran ƙarya ga jama'a
ii. Yin amfani da jama'a wajen neman ƙuri'a
iii. Rufa gaskiya game da shugabanci

**c. Siddabarun Addini**

i. Wasu suna amfani da sunan addini don tara kuɗi
ii. Yin sihiri ko rufa-ido a matsayin ibada
iii. Yaudarar mabiya

**d. Siddabarun Kafafen Sada Zumunta**

i. Shafukan boge (Fake accounts)
ii. Labaran ƙarya (fake news)
iii. Zamba ta yanar gizo (online fraud)

**e. Siddabarun Nishaɗi**

i. Siddabaru a fina-finai
ii. Wasannin sihiri (magic shows)
iii. Abubuwan kwaikwayo na ban mamaki

**Dalilan Yawaitar Siddabaru**

i. Talauci da neman rufin asiri
ii. Rashin ilimi ko fahimta
iii. Son arziki cikin gaggawa
iv. Lalacewar tarbiyya
v. Tasirin zamani da fasahar sadarwa

**Tasirin Siddabaru ga Al'umma**

a. Tasiri mara kyau

i. Rashin amincewa tsakanin jama'a
ii. Lalacewar tattalin arziki
iii. Ƙaruwa laifuffuka da damfara
iv. Rushe amana a siyasa da addini
v. Lalacewar tarbiyyar matasa

**b. Tasiri mai ɗan fa'ida (kaɗan)**

i. A nishaɗi da fim
ii. A koyar da ilimin kimiyya da fasaha

**Tasirin Siddabaru ga Al'umma**

Siddabaru yana da tasiri mai kyau da marar kyau, amma mafi rinjaye shi ne na illa:

i. Rage yarda da juna a cikin al'umma
ii. Lalata tattalin arziki ta hanyar damfara
iii. Yaɗuwar rashin gaskiya a siyasa da shugabanci
iv. Rushe tarbiyya da ɗabi'un matasa
v. Haifar da rikice-rikice da rashin zaman lafiya

Duk da haka, a wasu lokuta ana amfani da siddabaru a nishaɗi ko ilimantarwa (misali a wasan kwaikwayo ko sihiri na nishaɗi).

**Wasu daga cikin misalan siddabaru**

Siddabaru fasaha ce mai fadi wadda ta kasu kashi-kashi dangane da irin kayan aikin da aka yi amfani da su da kuma yadda aka tsara yaudarar idon. Ga wasu daga cikin fitattun misalan siddabaru da ake yi, tun daga na gargajiya har zuwa na zamani:

**Siddabarun Kayan Gida**

Waɗannan dabarun ne da ake amfani da abubuwan da ake gani yau da kullum don ba mutane mamaki. **Misali**:

**Karya cokali**: *Mai siddabarun zai nuna cokali mai karfi, sannan ta hanyar shafa shi kadan, sai cokalin ya fara lankwashewa kamar dalma.*

*Zobe a Cikin Igiyar Takalmi: Saka zobe a tsakiyar igiya wadda aka riga aka kullata, ba tare da an kwance kullin ba.*

**Baceccen Tawul**: *Sanya tawul ko tufa a cikin akwati ko tukunyar da mutane suka gani a matsayin wofi, sannan idan an bude sai a ga wani abun daban ya fito, kamar tattabara ko fure.*

**Siddabarun Katin Wasa**

Wannan shi ne nau'in da aka fi sani a duniya saboda saukin daukar katin a aljihu.

**Katin da ke Tasowa**: *Mutum zai zabi kati ya mayar tsakiyar sauran, sannan mai wasan ya sanya katunan a cikin kofin gilashi, sai katin da aka zaba ya fara tasowa shi kadai sama.*

**Sauyin Kalar Kati**: *Nuna katin bakikirin, sannan bayan an shafa shi da hannu sai ya koma "Heart" ja a gaban idon mutane.*

**Siddabarun Gargajiya a Kasar Hausa**

A cikin al'adar Hausawa, akwai wasu nau'ikan siddabaru da aka saba gani a dandalin wasannin gargajiya:

**Siddabarun Ruwa da Madara**: *Mai wasa zai kurbe ruwa sannan ya amayo da madara ko wani kalar ruwan daban.*

**Ciro Abubuwa daga Wuta**: *Saka hannu ko harshe a cikin garwashin wuta ba tare da an kone ba, ko kuma hadiye wuta.*

**Siddabarun Kwai**: *Sanya kwai a cikin hula ko tufa, sannan idan an girgiza sai a fito da zakara ko kaza daga ciki.*

**Manyan Wasannin Dandali**

Waɗannan suna bukatar manyan kayayyaki da kuma shiri na musamman:

**Yanke Mutum Gida Biyu**: *Sanya mutum a cikin akwati sannan a yanke akwatin gida biyu da zarto, sannan daga baya a sake hade su mutumin ya fito da ransa.*

**Tafiya a Kan Ruwa**: *Ganin mai siddabaru yana tafiya a kan ruwan tabki ko tafki ba tare da ya nitse ba.*

**Tashi a Sama**: *Sanya mutum ko wani abu ya rika shawagi a iska ba tare da an rataye shi da komai ba.*

**Siddabaru na dabbobi**

Yana daya daga cikin nau'ikan wasannin da mutane suka fi so, musamman saboda mamakin ganin dabba ta fito daga inda ba a tsammata ba ko kuma ta bace. A kasar Hausa da ma duniya baki daya, ana amfani da dabbobi daban-daban don nuna wannan fasaha.

Ga wasu misalan yadda ake yin siddabarun dabbobi:

**Fito da Tattabara**

Wannan shi ne fitaccen wasan da kusan kowane mai siddabaru yake yi. Yadda yake faruwa: Mai wasan zai iya kona wani kyalle ko takarda, sannan farat daya sai tattabara ta fito daga cikin hayakin ko wutar.

**Sirrin dake ciki**: Yawancin lokaci tattabarar tana boye ne a cikin wani aljihu na musamman a cikin rigar mai wasan. Tattabara tana da ikon zama a takure na dan lokaci ba tare da ta yi kuka ko motsi ba har sai an fito da ita.

**Zomo a Cikin Hula**

Wannan wasa ne na zamani wanda ya zama tamkar alamar siddabaru a duniya. Yadda yake faruwa: Mai wasan zai nuna wa mutane hula (top hat) cewa babu komai a ciki, sannan ya taba ta da sandarsa, sai kawai ya ciro zomo da kunnuwansa.

Sirrin dake ciki: Hular tana da karkashi na karya (false bottom), ko kuma akwai wani rami a kan teburin da hular take kai inda aka boye zomon.

**Canja Dabba zuwa Wata**

Wannan wasa ne mai ban tsoro da mamaki. Yadda yake faruwa: Ana saka kaza a cikin akwati, sannan idan an rufe aka sake budewa, sai a ga kura ko kuma kare ya fito.

Sirrin dake ciki: Akwatin yana da bangarori biyu (compartments). Daya bangaren yana dauke da dabba ta farko, daya kuma yana dauke da ta biyun. Ta hanyar juyawa ko zazzage wani katako, sai daya bangaren ya boye dayan ya bayyana.

**Muhimmancin siddabaru**

Siddabaru, a matsayinsa na fasaha da aka dade ana yinta a kasar Hausa da ma duniya baki daya, tana da muhimmanci ta fuskoki daban-daban, walau ta fuskar al'ada, ilimi, ko zamantakewa. Ga manyan muhimmancin da siddabaru take da su:

**Nishadantar da Al'umma**

Wannan shi ne babban dalilin yin siddabaru. Tana samar da farin ciki da nishadi ga mutane, musamman a wuraren taro kamar bukukuwan aure, shagulgulan sallah, ko wasannin dandali. Yadda ake rudar ido yana sanya mutane mamaki da annashuwa.

**Haɓaka Kaifin Basira da Tunanin Dan'adam**

Yin siddabaru yana bukatar lissafi, sanin yanayin tunanin mutane da kuma saurin lura. Ga mai yi: Yana koya masa yadda zai sarrafa hankali da dabarun magana.

Ga mai kallo: Yana sanya shi yin tunani mai zurfi don kokarin gano "yaya aka yi hakan ta faru?" Wannan yana motsa kwakwalwa.

**Tushen Samun Kudin Shiga**

Mutane da dama suna amfani da siddabaru a matsayin sana'a. Masu wasan kwaikwayo da "magicians" suna samun kudi ta hanyar nuna basirarsu a gidan talabijin, gidajen biki, ko wuraren shakatawa.

**Kare Al'adu da Tarihi**

A kasar Hausa, siddabaru tana daya daga cikin abubuwan da aka gada kaka da kakanni. Tana taimakawa wajen raba tsakanin abin da yake "tsafi" (maita/sihiri) da kuma abin da yake "dabara" (fasaha). Tana nuna cewa ba komai ne yake faruwa ta hanyar supernatural ba; wasu abubuwan dabarar hannu ne da hikima.

**Abin da bincike ya gano**

Wasu muhimman abubuwa da bincike ya tabbatar su ne:

1. Ruɗar Idanu da Kwakwalwa. Wannan yana nufin kwakwalwarmu ba ta iya ganin komai da yake faruwa a gabanmu lokaci guda. Idan mai siddabaru ya karkatar da hankalinka zuwa hannunsa na hagu, kwakwalwarka za ta "kashe" ganin abin da hannunsa na dama yake yi, koda kuwa yana yin hakan ne a fili.
2. Bincike ya nuna cewa abin da mai siddabaru yake fadawa masu kallo yana da tasiri sosai. Idan ya ce maka, "Duba wannan katin yadda yake canja launi," kwakwalwarka za ta fi karkata ga neman canjin launi, har ta mance da lura da sauran dabarun da yake yi da yatsunsa.
3. Binciken sun gano cewa koyar da yara masu bukata ta musamman siddabaru yana taimaka musu: Wajen inganta lafiyar jijiyoyin hannu. Wajen mu'amala: Yana sanya su samun kwarin gwiwar yin magana da mutane.

https://doi.org/10.66490/jajolls.2026.v10.i2.018

## MANAZARTA

Adamu M.T., 2014 Siddabaru a Kasar Hausa

Adamu, M.T. (1983). "Asalin Tsibbu: Yaduwarsa da Tasirinsa ga Al'ummar Hausawa". Kundin Digirin Farko. Kano: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Adamu, M.T. (1985). "Karya da Gaskiya a Ayyukan Tsibbun Hausawa." Takarda Wadda ya Gabatar. Kano: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Adamu, M.T. (1990). "Siddabaru a Kasar Hausa: Yanayinsa da Yadda ake Gudanar da shi". Kundin Digiri na Biyu. Kano: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Adamu, M.T. (2012). "Nazari a kan Bugun Kasa a Al'ummar Hausawa" Kundin Digiri na Uku. Kano: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Al-Ansari, J.M. (1956). Tarihul Mutanabbi. Beirut.

Al-Bakillani (B.S.) Miracle and Magic. Beirut.

Al-Falaky, T. (B.S). Sihri Harnuta wa ma'arruta. Beirut.

Bunza, A.M. (1990). "Hayaki Fid da na Kogo: Nazarin Siddabaru da Sihirin Hausawa. "Kundin Digiri na Biyu. Kano: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Bunza, A.M. (2006). Gadon Fede Al'ada. Lagos: Tiwal Nigeria Limited.

CNHN, (2006). Kamusun Hausa na Jami'ar Bayero. Zaria: Ahmadu Bello Uniɓersity Press Limited.

Dairaby, A. (B.S.). Mujairabatul Dairabi Alkabir. Cairo.

Daura, B. Isa, Y. Madauci, I. (1968). Hausa Customs. Zaria NNPC.

Gusau, S.M. & Funtua, A. I. (2010). Al'adu da Dabi'un Hausawa da Fulani. Kaduna: El-Abbas Printers and Media Concepts.

Joseph, G. (1959). The History of Medicine. Cairo.

Kirk-Greene, A.H.M. (1966). Hausa ba Dabo ba ne. Ibadan: OUP.